# SHAIDA CIKIN MINTI DAYA



DAYA DAGA CIKIN KAYAN AIKI
MAFI SAUKI NA SHAIDA BISHARA!

OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 1 1/23/25 5:25 PM

Allah yana so ya yi amfani da muryarka domin ya taimaki wadansu.



Kaunar Allah kyauta ce mai kyau, kuma yanzu kana iya raba ta da kowa.

Ko ba ka ji dadi ba da wani ya ba ka labarin Yesu ba?



Ko kana tunanin cewa Yesu yana son mu gaya wa mutane da yawa labarin kaunarsa mai girma?



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 2 1/23/25 5:25 PM

Wani yaro dan shekara bakwai, dan kasar Kenya, a nahiyar Afirika ya karanta wannan dan littafi mai suna *"SHAIDA CIKIN MINTI DAYA"* a gida. Da sati ya kewayo, yaron ya je makarantarsa ya raba shaidarsa ta minti daya tare da wasu abukansa biyar.

Ku yi tunanin abin da ya faru! Uku daga cikin abukan nasa sun yi addu'a sun bada rayuwarsu Yesu!

KAI MA KANA IYA YIN HAKANAN! Dukanmu muna da tarihi, kuma wannan *SHAIDA CIKIN MINTI DAYA* yana saukaka maka ka bada labarinka.

Yara da yawa cikin duniya suna shaidar bangaskiyarsu ta wurin amfani da wannan kayan aiki.






OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 3 1/23/25 5:25 PM

# NEMAN TAIMAKON ALLAH

Kowa yana son ya san ana kaunarsa. Saboda kana da kaunar Yesu a cikinka, suna so su saurare ka ba su labarin kaunar tasa.



Ka roki Allah ya taimake ka ka ba su labarin kaunarsa. Kana iya kowace rana ka fara da wannan addu'a mai sauki:

**"Ya Yesu, in ka yarda ka yi amfani da ni yau domin in taimka ma wadansu su san kaunarka mai girma. Amen."**





OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 4 1/23/25 5:25 PM

## KAYAN AIKI NA BADA SHAIDA CIKIN MINTI DAYA

1. IZINI

   "KO ZAN IYA AZA MAKA TAMBAYA?"

2. (K.K.) KAFIN IN SAN KIRISTI

   "AN YI WANI LOKACI CIKIN RAYUWATA INDA..."

3. (S.) SAKEWA

   *KA BADA TARIHIN YADDA KA JI LABARIN KIRISTI*

   "SAI WATA RANA,..."

   DA NA JI CEWA YESU YA MUTU DOMIN ZUNUBAINA

4. (B.K.) BAYAN DAUKAR KUDURI

   "TUN DA NA KARBI YESU, NA..."

5. "INDA BAN KARBI YESU BA, DA NA..."



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 5 1/23/25 5:25 PM






OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 6 1/23/25 5:25 PM

# IZINI

Idan muna neman izini wurin mutane, muna nuna masu ladabi. Kuna iya farawa da

**"KO INA IYA AZA MAKA TAMBAYA?"**

Idan sun yarda, sai ku aza tambaya kamar haka

**"MINE NE ABU MAFI MATUKAR FARIN CIKI DA KUKE TUNE DA SHI CIKIN RAYUWARKU?"**

Bayan sun fada maku abin, ku tambaye su da cewa

**"KO INA IYA FADA MAKA ABIN DA KE MAFI MATUKAR FARIN CIKI A RAYUWATA?"**

Idan suka ce i'i , kenan sun ba ku izini ku bada labarinku. Ku takaita shi. Cikin minti daya kuna iya bada labarin yadda Yesu ya sake rayuwarku!

**YANZU LOKACI NE NA KA BADA TARIHINKA...**



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 7 1/23/25 5:25 PM

# (K.K) KAFIN IN SAN KIRISTI



8.

## Dukanmu muna da wani tarihi kafin mu sadu da Kiristi.

Yaya rayuwarka ta kasance kafin ka san da cewa Yesu yana kaunarka?

Watakila kana cikin kadaici ko kana jin tsoro. Watakila kana cikin bacin rai ko cikin hasala. Watakila kana yi maka iyayenka rashi biyayya, kuma kana fada ma mutane miyagun maganganu.



Takan yiyu ba ka tuna da wani lokaci inda ka roki Allah ya gafarta maka ba. Watakila ka tuna da bukatar samun gafara ko taimako domin ka daina aikata wasu miyagun ayyuka.

Yi tunani a kan kalma uku domin ida wannan hurci (page 16):

"An yi wani lokaci cikin rayuwata da..."



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 9 1/23/25 5:25 PM

# (S) SAKEWA



10.

OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 10 1/23/25 5:25 PM

# A WANE LOKACI NE KA SAKE?

Kowa yana da lokaci a cikin rayuwarsa inda yake tunawa da Allah. Wane ne ya taba baka labarin Yesu?
Ga misali:

"Wata rana wani ya ba ne labarin irin yadda Allah yake kaunata sosai. Da dadewa ya aiko da Dansa Yesu daga sama ya zo ya rayu tare da mutane a nan cikin duniya. Ya kaunaci mutane, kuma ya warkar da marasa lafiya. Ya mutu domin zunubanmu da kurakuranmu, AMMA SAI bayan kwana uku ya tashi daga matattu domin ya tabbatar da cewa lalle shi Allah ne.
Da na ji Yesu ya mutu domin laifofina, kuma ya tashi daga matattu, sai na roke shi ya gafarta mani, ya kuma shugabanci rayuwata har abada. Wanna shi ne lokacin da **na sake**."



Mi ka roka Allah ya yi maka?
Rubuta shi a shafi na 17.



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 11 1/23/25 5:25 PM

# (B.K) BAYAN DAUKAR KUDURI



12.

# BAYAN DAUKAR KUDURI

## "Tun da na karbi Yesu, na..."

Yanzu sai ka fada masu kyakkyawan abubuwa da Yesu ya yi maka. Ya ba mu sabuwar murna, sabbin abukai, kaunar Allah, gafara da kuma alkawarin wata rana za mu je sama.

**"Tun da na roki Yesu ya gafarta mani, ya kuma shugabanci rayuwata, ina da sabuwar kauna cikin zuciyata, sabon bege da alkawarin zan je sama wata rana in rayu tare da Yesu har abada!"**



## Wadanne abubuwa uku ne masu kyau da Yesu ya yi cikin rayuwarka?

Ka je a shafi na 18 idan ka samo amsohinka.



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 13 1/23/25 5:25 PM

INDA BAN KARBI YESU BA, DA NA...



14.

## "Inda ban karbi Yesu ba, da na..."

Wasu mutane da ba su karbi Yesu ba, suna tsoron kadaici, ko suna aikata miyagun abubuwa. Rayuwarsu daban ce, saboda ba su san Yesu ba.

**"Idan ban karbi Yesu ba, da na rayu cikin bakin ciki."**



Ta wurin bada tarihinka, kana nuna ma abukanka yadda Allah ya sake rayuwarka. Yanzu lokaci ne da za ka tambaye su idan suna son su bada rayuwarsu ga Yesu, su kuma roki Allah ya gafarta masu. Idan ba su a shirye su yi addu'a, kana iya ka tafi gida ka yi addu'a dominsu. Ka bari su ma Allah ya yi masu magana kamar yadda kai ma ya yi maka. Idan suna da tambayoyi, kada ka ji cewa dole ka iya bada dukan amsoshi. Sai ka gaya masu abin da Yesu ya yi cikin rayuwarka kadai, da kuma dalilin da ya sa kake kaunarsa.

Rubuta amsoshinka a shafi na 19.



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 15 1/23/25 5:25 PM

K.K.

# KARE WANNAN HURCI DA KALMA UKU KO FIYE:

**"AN YI WANI LOKACI CIKIN RAYUWATA INDA..."**

1.............................................................................

2.............................................................................

3.............................................................................



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 16 1/23/25 5:25 PM

5.

# A WANE LOKACI NE KA SAKE?’

1. YAYA KA JI LABARIN YESU?

“SAI WATA RANA,...

..................................................................................

..................................................................................

..............................................................................”

2. CIKA WANNAN HURCI:

“DA NA JI YESU YA MUTU SABODA ZUNUBAINA, YA KUMA TASHI DAGA MATATTU, NA GAYYACE SHI YA...

..................................................................................

..............................................................................”



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 17 1/23/25 5:25 PM

B.K.

## WADANNE ABUBUWA UKU NE MASU KYAU YESU YA YI CIKIN RAYUWARKA.

**"TUN DA NA KARBI YESU, NA..."**

1. ................................................................

2. ................................................................

3. ................................................................



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 18 1/23/25 5:25 PM

## YAYA RAYUWARKA ZA TA KANSANCE IN BANDA KIRISTI?

"INDA BAN KARBI YESU, DA..."

..........................................................................

..........................................................................

..........................................................................

..........................................................................

..........................................................................



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 19 1/23/25 5:25 PM

# JE KA DA ZURFI

Bayan da ka bada shaidarka cikin minti daya, kana iya ka tambaye su idan suna so su san yadda za su tabbatar da cewa za su je sama."

Idan amsar "i'i" ce, to sai ka fada masu matakan samun ceto.

1 - YARDA Na yarda da cewa na yi laifi, kuma zunubaina sun raba ni da Allah mai tsarki. (Romawa 3:23)

2 - GASKANTAWA da Yesu Kiristi ya mutu kan giciye domin ya gafarta mani zunubaina, ya kuma tashi daga matattu domin ya tabbatar da shi ne Allah kadai na gaske. (Romawa 10:9-10)

3 - TUBA daga zunubai gaban Yesu, da rokon sa ya gafarta mani. Na roke shi ya shugabanci rayuwata har abada. (1 Yohana 1:9)

Idan sun gane matakan, sai ka tambaye su: "Ko kuna son ku roki Yesu ya gafarta maku, kuma ya zama shugabanku a yau?"



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 20 1/23/25 5:25 PM

# KARE TARIHINKA

Idan suna son su yi addu'a tare da kai, sai ka ce su maimaita wannan addu'a da babbar murya, ta wurin amfani da matakan da suka koya masu, ko kuma 'Waken Ceto" (shafi na 22).

**"Ya Yesu, na yarda da cewa na yi laifi, kuma ina tuba daga zunubina. In ka yarda, ka yi mani gafara Na gaskanta ka mutu domin laifofina, ka kuma tashi daga matattu. Na tuba daga zunubaina, kuma ina rokon ka ka zama shugabana. Ina kaunar ka Yesu! Amen."**



Idan suka kare addu'ar, sai ka yi masu barka, ka kuma ce su yi abubuwa uku masu muhimmanci: karanta Littafi Mai Tsarki kowace rana, yin addu'a kowace rana, da zuwa majami'a kowane lahadi. Bayan wannan sai ka lisafta su cikin abukanka.



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 21 1/23/25 5:25 PM

# Waken Ceto

Yesu, ka mutu kan giciye
Ka tashi daga matatu domin ka ceci batattu
Ka gafarta mani dukan zunubaina yanzu
Ka zo ka zama Mai Cetona, Ubangijina, da Abokina
Ka sake rayuwata, ka sabunta ta
Ka taimake ni Ubangiji, in rayu dominka.

Ku saurari wakar a cikin
ONEMINUTEWITNESS.ORG

The Salvation Poem.
Written by Matt and Sherry McPherson.
© 2004 by The Salvation Poem Foundation, Inc.
ALL RIGHTS RESERVED.
WWW.THESALVATIONPOEM.COM



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 22 1/23/25 5:25 PM

# HUSAHU DOMIN MASU KOYARWA

1. Gabatar da **TAUSAYI** daga Matta 9:36.
2. Bada MINTI 1 **domin hadace yatsu** 5 (shafi na 5).
3. **Koyarda SHAIDA CIKIN MINTI DAYA, yatsa daya bayan daya:**
   - Karantawa daga cikin dan littafi mai alamun yatsa biyar.
   - Ku bada shaidarku dangance da kowane yatsa domin kowa ya ji.
   - Kowa ya rubuta shaidarsa. Ku bada minti daya na shiru.
   - A saurari mutum 3, domin kowa ya ji abin da suka rubuta.
   - Kowa ya raba da abokinsa abin da ya rubuta.
4. Ku bada shaidarku kowa ya ji.
5. Ku ce kowa ya raba shaidarsa da abokinsa.
6. A sake raba shaidar da wani aboki daban.
7. A aza tambay 3:
   a. Mutum nawa suka gane ma'anar *SHAIDA CIKIN MINITI DAYA*?
   b. Mutum nawa ke iya amfani da wannna kayan aiki bayan wannan koyaswa?
   c. Yaushe ya kamata mu fara amfani da wannan kayan aiki—badi? Yaushe?
8. Bada umurni domin **AIKATAWA**: A karfafa yara sur aba wannan da mutanen da ke kewaye da su, da cikin makarantu kowace rana. Ku sami lokacin balaguro tare da manyan mutatne, ku same su biyu-biyu, ku raba shaidarku ga a kalla mutum 4 (sani babu aikatawa banza ne).
9. Bayan da sun raba shaidarsu, a tambayi mutum uku su bada nasu tarihin.
10. ***KALUBALAR KWANA 21*** - Ku ce su raba shaidarsu tsawon kwana 21, ku kuma kira /ko ku aika sako ga abokinsu domin ku karfafa su.
11. A sake koyar da su kowane wata, a ba yara wasu abokai daban.



OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 23 1/23/25 5:25 PM

Idan kuna so ku sadu da wadansu da suke son su karfafa bangaskiyarsu, sai ku same mu a:

**WWW.*ONEMINUTEWITNESS*.ORG**

AKWAI KYAUTAI: ***OASISGIFTS*.ORG**



*LITTATTAFAI, WAKOKI & KAYAN AIKI MASU KARFAFA SHAIDARKU!*

Ku shiga yanar gizonmu domin ku sami sako daga SHAIDA CIKIN MINTI DAYA kowane sati. Wannan za ya ku zarantar da ku domin abubuwan da za su dawwama... rayuka!

Domin odar littafin *SHAIDA CIKIN MINTI DAYA™* sai ku rubuta mana ko ku kira mu a:

Oasis World Ministries
PO BOX 58 CHAMPLIN, MN 55316 USA
763-425-9355 | info@oasiswm.org

Oasis
WORLD MINISTRIES

© 2019, Oasis World Ministries. Written by Tom Elie and Oasis World Ministries. All rights reserved. No part of this booklet may be changed in any way or reproduced in any form without written permission from Oasis World Ministries. V15UDT58 CHILDREN'S HAUSA

OMW_3.5x4.25_for_V18UDTW_HAUSA_Booklet.indd 24 1/23/25 5:25 PM